# Ka Dage Domin Bauta ta Gaskiya (Sashe na 1)

An dauko daga babi na 16 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?* za a iya samunsa a dandalin jw.org/ha.

**MANUFA: Ka bincika abin da ka yi imani da shi da kuma dalilin da ya sa ka yi hakan, kuma ka bincika abin da Littafi Mai Tsarki ya koyar don ka iya bayyana wa wasu abin da ka yi imani da shi.**



## ME AKE NUFI IDAN AKA CE YA KAMATA MUTUM YA BAUTA WA ALLAH DA GASKIYA?

### 1 KA BINCIKA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

Me kake ganin wasu mutane za su ce?

______________________________

______________________________

Me *ka* yi imani da shi?

______________________________

______________________________

Me ya sa ka yi imani da hakan?

______________________________

______________________________



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 2 KA BINCIKA ABIN DA LITTAFI MAI TSARKI YAKE KOYARWA

**Idan muka yanke shawarar bauta wa Jehobah, hakan yana nufin cewa za mu ƙudura niyyar bauta wa Jehobah Shi kaɗai da dukan zuciyarmu.**

(Ka duba babi na 16, sakin layi na 1-5 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

**Karanta Fitowa 20:4, 5 da 1 Yohanna 5:21.**

Mene ne aka faɗa a waɗannan ayoyin da ya nuna mana yadda Allah yake ji idan muna yin amfani da sifofi a sujjadarmu?

_______________

_______________

_______________

**Karanta Kubawar Shari'a 18:10-12.**

Mene ne waɗannan ayoyin sun koya mana game da yadda Allah yake ji idan muna bauta wa kakanninmu?

_______________

_______________

_______________



**Kamar yadda ba za ka sha alawar da aka ɗauko daga bola ba, haka ma bai kamata ka yi bukukuwan da arna ne suka soma**



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## Idan muna so mu bauta wa Jehobah da zuciya ɗaya, wajibi ne mu daina yin bukukuwan da Allah ya haramta.

(Ka duba babi na 16, sakin layi na 6-12 na littafin nan *Menene Ainihi Littafi Mai Tsarki Yake Koyarwa?*)

**Karanta Farawa 40:20 da Markus 6:21.**

A cikin Littafi Mai Tsarki, an ambata mutane biyu ne kawai da suka yi bikin ranar haihuwarsu kuma mutanen ba sa bauta wa Allah. Me ya sa aka ba mu labarinsu?

______________________________________________

______________________________________________

______________________________________________

______________________________________________

**Karanta Ishaya 52:11 da Afisawa 5:10.**

Me ya sa ya dace mu san tushin ranar bukukuwan da mutane suke yi?

______________________________________________

______________________________________________

______________________________________________

______________________________________________

Me ya sa zai yi kyau ka kuɗiri niyyar dage domin ibada ta gaskiya?

______________________________________________

______________________________________________

______________________________________________

______________________________________________



www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania

## 3 KA BAYYANA ABIN DA KA YI IMANI DA SHI

IDAN WANI YA CE…

**Ba na *bauta* wa sifofi, amma suna taimaka min in kusaci Allah sa'ad da nake addu'a.**

ZA KA IYA CE…

**Ya yi kyau da kake so ka kusaci Allah ta wurin addu'a. Amma yin amfani da sifofi wani batu ne dabam domin…**

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?

IDAN WANI YA CE…

**Babu mutumin da yake bikin ranar haihuwa ko kuma ranakun hutu don arna ne suka soma bikin, amma waɗannan bukukuwan suna sa iyalai su kasance tare.**

ZA KA IYA CE…

**Yana da muhimmanci iyalai su kasance tare. Duk da haka, yana da kyau mu san dalilin da ya sa ake bukukuwan nan domin…**

Wane nassi ne za ka iya karanta wa mutumin?

Bisa ga ra'ayin mutumin, ta yaya za ka bayyana wannan nassin?


www.jw.org/ha © 2017 Watch Tower Bible and Tract Society of Pennsylvania